[8/19, 10:08 AM] Haisahhtttttt💅: *👠👠💅BAGIDAJIYACE👠👠💅*

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION.*
*(Home of peace ,joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

*Godiya*
Ina mika godiya ta ga Allah madaukakin sarki,mai kowa da komai wandaya bani lafiya da Aron numfashi,har nafara kawo maku sabon  wannan littafin nawa ,Allah nagode maka.Allah kabani ikon ga mashi cikin koshin lafiya,kuskuren  dasuke  ciki Allah kayafe mana.Ammen

*Dedication*
Na sadaukarda pajinnan gareku  masoyan littafin RAYUWAR AFREDARH, Allah yabar kauna...🤍🖤💜

*GARGADI*
Wannan littafin 'kagaggene daga kwalwar Hassenart ,idan kinga yayi daidai da rayuwarki  ,to kisani arashine.don haka vanyarda ajuyamun littafina ta kowacce sigaba batareda izininaba,yin hakan babbar zunubine...akiyaye

*_written_ _by_*
 *_Hassenart_ _Mohammed_*

*Litattafan marubuciyar:-*
-RAYUWAR AFREDARH (endless love)
-QASAITATTUN MATA
-RAMUWAR GAYYA (The shaded blood)
Now
BAGIDAJIYACE

*Wannan littafin na kudine,adon haka za'a biya #200 na katin mtn ma wannan number 09065990265 sai ayi screen shooting as evidence a dai turama number na saman.vip kuma #300 don haka biya kudinki ki karanta littafin ki hankali kwance🤗🤗 wacce tabiya kudin ramuwar gayya nayi maku rangwamen  zata biya #100 ne  amaimakon #200 inkuma

VIP ne #200 a maimakon #300*

Bismillahir~ rahmanir~ raheem

---

1&2

*Kauyen fallankin malam yahaya*
*Zuntu*

Wani irin gudu takeci  uwa rainta zai fita,sakamakon ganin 'yan kungiyarta suna dab da shigewa rutsutsin wajen gonakin.kwalla ma daya daga cikin su kiratakeyi da karfi, hakan yasa suka dakata  da tafiyan.
Har ta Karaso cikeda haki
"K'ure dadi nine zakuyiwa wulakanci ko?,wato da bansauriba tafiya zakuyi kubarniko?"

"Laa bahaka bane indo kinsanifa sarai lokacin birek gajerene...gashi munada yawa masu cin gwavan  inba muje da wuriba za'a iya komawa aji ,ko masu gonan su zo"

"Wooo, kahe  da sunhememu...hanzarta mu higa layi yanda akasa ba ,kasan gonan nan akwai hi da hammatsi" tafada da lalataccen hausan ta na gidadawan 'kauye
Layi maza uku sukayi agabanta sai rahane kawarta ta biyar sauran mazan abayansu
A hankali take tafiya sadaf sadaf cikeda tsoron karta taka kan maciji...har suka iso fili suka fito sosai iya ganin ka mai cikeda bishiyoyin mangoro da guava
Daf  undo tahaye nagovan tana watse masu suna watsawa abuhu

Dagacan  nesa wani mutumi dake gyangyadi karkashin bishiya da zugegen dorina a gabansa, ga dukkan alamu maigadin wajen ne,ya hango su a hankali yashiga sad'ad'awa wajenda suke,karaf kan idon indo,dirkowa tayi akan bishiyar jikake tif!

Hada baki sauran sukayi suna fadin "lafiya?"
Ai yankan hanya tayi da gudu tana gayamasu cikib waka faditake"ga mai gona ga mai gona nan...Wanda yakalla banyafeba".
Haba kafa mai naci banvakiba,shimako maigadin  yadade masu baya .gudu sukaringayi tun

suna jin nishad'i har indo  tafara kuka ,tuni a hanyar sun zubarda buhun goban amma mutiminka yaki daina binsu, har suka shiga filin makarantan yana binsu.daidai nan aka kada kararrawa na komawa aji, ai dagudu suka hade da yara kowa yayi ajinsu.

Koda maigadi yaga sun tsira ,takaicin gudun da yayi yakeyi,atake  yayanke shawarar tafiya ofishin malamai yakai kararsu
Duk ko malaman  suna nan...
Discipline master ne yamike  cikeda fushi yacewa mutumin "yi hakuri malam ,yanzu duk sun gama shiga aji don haka muje inzaja iya ganesu a tsintosu"

"Tabbas zangane ,wannan mai muryar chanisawan(yana nufin indo)

Aji aji yaringa zagawa dashi ,har sukazo js 3 anan tun kafin sushigo yayi idobiyu da idon indo ta windown ajin ,ido  ranbadadau da kwalli. Daganinta kaga Mara gaskiya.

" malam itace wagga"yanuna ta da yatsa da sauri
Malamin bai wani damuba don yasan indai indoce zata aikata  abunda yafi haka

"Fito gaban allo kowa yaganki  barauniya,ina sauran?" Cewar discipline master.

Ganin ba matsera  yasa tafito tana muzurai,kyar tayi da ido ma en ajin
"K'ura dadi,lafazi,rahane....kai nagaji  dakiran sunayenku,malamai ai he kuhito ko"
Ba arziki suka yo waje ,don sunsan inya zakado su zafa  adake sun,sukuma bi hanya itama ta narka.
 dukansu saida suka fito malamin ya mikama  maigona bulala yazanesu...haba kura dadi yafara gaba shine dama bai tsoron bulala, sauke masa da yafara yi ,azabar dukan  yagigitashi kwara ihu yakeyi iya karfinsa,tuni idon indo ya raina fata,baya taringa yi har tajingina da gajeran windon  ajin basu yi auneba saidai sukaji dirkanta cikin gonakin bayan ajinsu,kalkalawa tayi da gudu 'yan ajin akasa sukabita amma haka suka kare gudun su suka dawo don tab'ace masu.
Dabalain gudu tashiga gidan,mama na tsugune tana wankin  waken alala  bataji shigiwarta ba saidai taga giftawarta tayi ciki da roban waken.
Mikewa mama tayi tana tafa hannu tareda sallallami
"Auta wa kuma kika tono  yau ?ina makarantab?kifito inji nace"

"Alkur'an mama banfitotwa sukamani....ke makarantan ma anbari daga yau...yasin yau ban kwanan garin nan tunda kowa ya tsaneni"

Shigowa dakin tayi ,taciro ta a bayan kofan.
"To kwantarda hankalinki kimun bayani sosai"
Hmmm inazuwa " randa tanufa ta dibi ruwa a mod'a tashiga kwankwa'da daga nesa kanajin karan wucewar ruwan.tana gama sha ta suri  buta taje bakin vandakin gidan ta tsula fitsarinta yako  gangaro wajen dakin yaya(kishiyar mamanta)ta kakkabe jikinta tashigo daki.
Mama nanan zuru tana jiran  fitowa r ta, zama tayi kan tabarma gefen mama tayi gyaran murya

tasoma koromata bayani

"Mama ina gonan gobannan danake kawo maki kinaci ,kina tond'e baki?todai yau dubunmu tacika dinko su rahane yau sunkade har buzunsu da duka...."

"Ke tsaya auta menene na duka kusiya Abu da kudinku?"

"Tab lallai ma to debosu mukeyi ,hannu nki ana ke hin dauka kudi muke basu to yasin yau ban zaman garin nan Zaria ba nufa gidan anty,bazan zauna me gari yazo akamoniba,dama gashi da jikakka tsakanina dashi....ki tashi ki shirya mun kaya don alkuran akazo kamani zance kece barauniyar zaunen ,akama dake..."

"Auta nice barauniyar ?to ba inda zaki kijamasu magana ,acan su basu saba da hayani yaba ,unguwarsu na natsatsune"

Geiwoyinta tasa a kasa tana rokonta "mama nice fa autarki indo,zakiso akashani,ji nake idan na kara kwana ajalina kekira ,konafada ruwa ko rijiya...

.....to shahararriya  fito ki wanke fitsarin da kikayi ....ace kaf  ,kafin gidannan kin karyesu da fitsari?komai nagida kin lalaceshi ,mudai  anhaifo mana annoba"
"Bani bace annoba sunusi danki shine annoba"buge bakinta mama tayi,tasoma ba yaya hakuri

" yimana shiru baqar algunguma...ba kece kikajaba,to maza sata  tawankemun kofar daki don bazan dauki cin kashiba"Tsidik tayi mata a gaba
"Ninan na isheki ,kuma tunda kika zagi uwata abakin wankin  fitsarin kofar dakin ki"
Tayi shigewarta muryan daki tahaye gado,masifa taringa yi kamar zata ari baki tagaji tafita ,don takaici ya hana mama bintu magana.saida taji tsiyar ya kwanta,tashiga tasameta tayi daidai a gado tana barci hankali kwance.daka Mata duka tayi acinya
"Jai'rah tashi ki hada kayan ki kitafi zarian,konaji kunne na kwana biyu"
Aidasauri tafigi Ghana mustgo tagaudanna kayanta acikin.taje tadako  tsaminta tadan gurza Vaseline guburi guburi,tayafa kanannadadden mayafintada kila baitava ganin iron ba a rayuwar sa
"Mama na shirya sallameni,karsu taso makarantan" tsaki tayi ta kwanto hannun zani taciro Dari biyar tabata,tashi ga rumbu ta jibgo kayan tsaraba  irin nasu na 'yankauye tabata takai masu.mai baro tafita tanemo  ya kwashe kayan ta suka tafi tasha,saida tajita a motar Zaria .kuma tacika  sun hau kwalta  tafara jin daidai a ranta"cab ai Yaseen sai na huta na watanni zandawo lokacin komai ya lafa...,"tunanin rayuwar ta data gudanar a garinsun yasoma dawowa kwanyarta,tartar.........

#vote
#share
#comments

[8/19, 10:09 AM] Haisahhtttttt💅: 👠👠💅BAGIDAJIYACE👠👠💅

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace, joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

Wannan pajin nakune kuyi duk yanda kukaso dashi,,, kawayena,aminan arziki,abokan tsegumi da dan gulma🤪
Aisha Abubakar musa(mrz zuntu)
Zainab Isah (hajiya babba)

Written by✍🏻
Hassenart Mohammed😘

Littafan marubuciyar:-

-RAYUWAR AFREDARH (Endless love)

-QASAITATTUN MATA

-RAMUWAR GAYYA (The shaded blood)

_And now_

BAGIDAJIYACE

*littafina dashi da ramuwar gayya,dukna kudine#200na mtn ake biya ta wannan number 09065990264 inkuma vip kikeso zaki turo #300 👷ace tabiya na ramuwar gayya kuma #100 zata biya VIP #200 炮ajiya daure rage ciki kibiya ba tsada bane gareshi da zaisa sai anfita  maki dashi kina jira aturo kisamu, inmai turowa hidima  yasha masa kaifa🙃😏*

3️⃣-4️⃣

Wani handsome sojane  fari tar kyakyawa ajin farko sanye cikin farar T-shirt da gajeren wandon kakinsu, nagani tsaye acikin filin wajen training din  'yan Navy acikin makarantar NDA ta kaduna,gadai dukkan alamu dalibin department dinne .waya yakeyi cikin natsuwa...ayanayinsa da yanda yake harhad'a maganarsa zakagane shid'in bamai cika son hayaniya bane,da yawan surutu....
daidai nan wata matashiyar inyamura takaraso wajen dayake itakuma cikin complete shigan uniform dinsu na navy,amma tana d'auke  da alamar 'yan shekaran farko,acikin collegin.

Tana ganin sa ta fara feck call,"hello my friend,can u hear me?...eh I told u what man can do,a woman can do beyond... Letz..."rashin sani kenan donko
Awani bala'in zuciye  yaje ya shaqota ya jefata cikin wani tabon  jar kasa mai dauke da ruwa kimbul,tako  fada ta fuska, ji kake facccch!, yayi saurin bin bayanta kafin ta dago yataka keyarta fuskarta dakanta yalume cikin ruwan jar kasan mai kamada yanbu na training dinsu.haba wutsil witsil takeyi da kafa kamar kifi, tana kuka amma bakaji saima ruwan dake shigamata ta hanci da baki,adole tai shiru cikin sadakar da cigaban rayuwa.shikan gogan ko a jikinsa saima yacigaba da wayarsa.

Da sauri wani matashin sojan ya 'karaso wajen dasuke,rai a 'bace ya saita cinyar kafar da ya daura akanta ,ya kaimasa tokari da sauri yad'an  goce, cikin sauri yayi azamar janyota ya watsar gefe,sannan ya soma magana
"Farouk yaushe kazama maras imani ?,kashata zakayi komene,jibe tafa wannan tama suma...taimaka mukaita asibiti"

"...kai baka da hankali,nine zanyi punishing mutum kuma inzo inkaishi inda zai samu relieve?... Bayan rashin kunyarda victim din taimun?Towaima me ruwan ka dani da zaka daka tar dani eyee haidar?,kamata yayi kabarni inbata lesson tukuna,i want to confirm her that,what man can do, a women can never ever do...even if they can die and resurrected hundred times,so now banwaje mtseww"
bai jira tacewarsaba ya ja tsaki ya bar wajen.girgiza kai aliyu yayi ,yakira juniors dinsu dasuka zo wucewa yasa suka taimaka suka dauketa  zuwa asibitin cikin makarantan.

**********

Indo kam an sauka a tashar kofar doka cikin zeetown lafiya, mai Babur tayi kiran sa tayi masa kwatancen inda zai kaita ,yadaukar mata buhun tsara barta,yasa agaba , tsohon Ghana must go dinta abaya sannan itama tahaye bayan.tiiiiiiii haka yakwasheta har GRA .daidai kofar wani

gida dayafi  duk sauran gidajen gurin tsaruwa ya ajeta ,taciro #200 tabasa yanda sukayi ciniki,kamar mumina Wanda tasaba  biyar masu ocada hakkinsu,yo ehmana matarda  saidai ta dirka tafalla a guje tace inkanada zarra kabiyota ka amsa?!

Tadad'e  tsaye kafin tasami  almajiri tarokesa ya shigar mata da kayan.
Tundaga bugun gate d'in, gatemen din su kasan sunyi ba'kin mahaukata.
Don haka dasauri nakusada kofar ya bude cikeda fushi dafatan  kama kowaye ya Zane....ganin ta yasasu saranda  don yasan watan  aikin su ya tsaya,baxai taba manceta da balainta ba,sakin baki yayi galala yana istigfari aransa inyayiwa Allah laifine  ,donko  hadaka da indo gida daya babbar jarabawace..."
Bai ida  zancen zucinba yaji takarashe hankado gate din ji kake,garararaf to ufo ciki abunta,a firgice ya juyo yana kallonta
"Malam inkagama kalle kallen ba yaro waje yahuce,haba mutum haka sai kallon tsiya ba aiki?, Sam anty bahuyi sahan  mai gadiba...wannan ai shai  yarinka koron masu bakin alkhairi"
Fuuuu tayi ciki da katon ghana mustgo dinta akai.
Dasauri ya amshi buhun hannun almajirin,yabi bayanta dashi don Sam baiso yazama na farko dazasuna soma rikici.

Babban kofar dazai sadaka da asalin cikin gidan tashiga kai tsaye,tasoma kwarara sallama
"Assalamu alaikum sallama nake,gaba kuwa gaisheku  take,ina  antyn tambayrku nake"
"Barkanki  da zuwa...anty na ciki" taron masu aikin suka hada baki wajen bata amsa.
Cikeda fargaba  daya daga cikin housemaid din ta amsheta da Jakarta ,har cikin falon.
ACikin falon ,Hassana da Husseinane zaune akan kujera Hassana game take a laptop dinta Hussaina na charting da wayarta  ta like kunnenta da earpiece, sai Ahmad dan karamin kaninsu dabazai gaza 10years ba,dake kan dinning yana shan Golding morn.ga karan t.v dayacika falon ,din haka Sam basu ji shigowar taba saidai sukaji dirkan buhu  akan center Carpet din ,take kurar  kuka da barkonu yatashi  alamun  sun fashe ta cikin buhun.daidai nan indo tasoma magana
"Kai dan uwarku  bakuga  muhane bane hiyyeee"
Ai tari  suka dauka atare,don Hassana harda hawayen azaba don direct yawuce mata ta kofofin hancinta.
dasauri tarufe laptop dinta tabar shinan tahaura sama da gudu,sauran 'yan uwannata suka dafe mata baya

Tsaki tayi tasama  kujera tabaje tanajiran azo atarbeta,shiru har kusan Rabin awa. Sannan ne Hassana tadawo falon,tasungumi laptop dinta tanufi  hanyar komawa dakin su

"Ke ina  uwartakune,ne ne?"
"Kai indo kin cika fitina to tana dakin abbey kuma har yanzu ba tafito ba tukun, sai kijira in akayi azuhur zasu fito ai"

"Caftsi,kenan zaman cikin nan zantayi?,aiko na gaji  saidai ko naje  dakinku najirata....yaa shafii

kafii" takarashe maganar ta tareda yunkurawa tayi hanyar wajen steps din.Ai azabure Hassana tayi ciki da gudu kamar wacce ta ga horror, tashige dakin su tamurza key da sauri.
Jingina tayi da jikin kofar tana hakiiy.

"Ke lafiyarki kuwa?" Hussaina takaraso tana tambayarta

"Inafa lafiya, laluwa bala'i zata shigo mana daki"bugun kofar suka somaji da karfi
"Mtseww to meye ?,ke wannan tsoron ne zaisa tarainaki....kina ganinta da lodin kayannan ,kinsan tafiyanta ba yanzuba...kuma kinsan abbey baison hayaniya ,ji yanda take bugun kofa?"
Janyeta tayi ajikin kofar tamurza key din ta bude tashigo,duk suka koma gadon su suka zauna

"Ke to meye na guduwa ,harda sa makulli saikace kinga mu da fatalwa?"
Hussaina ne tasoma magana cikeda kambamawa
"Wanemu anty ayeeshar...jakadiya er saleh,sa baki dariya sai yak'e ,kowa yace zaiga dariyansa ya mutu ,margamargan dutse kinfi gaban aljihu....barkanku da zuwa bakin zuntu"...........

" aiho ai na aza baku marhabin danine ,dasaina koma inda nafito ".
Allahumma ameen, Hassana tace a hankali

" wanemu anty ,salan kija mana fushin ummy....ai murnar ganiki muke...(ta waigo da fuskarta wajen Hassana) ai ma ringa samun dadadan labaran ban dariya awajeta ko !"

Gyada kai tayi kawai batace komaiba.turo kofar akayi,ummyne da abbey suka shigo yi mata sannu da zuwa,din dinki shigewarta

"Barkaana ,barkaana daganinku mutanen zuntu...kun iso lafiya?"
Dadyne yake magana tareda tafa hannu wa fuskarsa cikeda fara'ah

"Barkankadai alhajinsu 'yan biyu...munsameku lafiya"
"Lafiya klou,ya wajen su mama....Hassana yabakusata tai wankaba"ya tambaya cikin sigar tsokana

" yoooh inbanda abinka alhj yazasu martaba ni ,haikashe fatsima uwarsu?...dadai itane zasu bata...to kusani matsayin mu daya da fatsime dan iyayen Ku,gatanan tsaye Ku tambayeta "tafada tana zazzare ido kamar uwarsu

" ayi hakuri dai ranki yadade...kuruciyace"abbah yafada cikin sugar zolaya dafatan kwantarda tarzoma

"Hmmm...wai ina mutumina ne aliyu haidara,hoja mazan hwama" tafada tana washe dafaffun hakoranta

Ummyy ta amshe maganar"Nana aisha tashi muje dakina ...sweetheart kubiyota da Jakarta...aliyu na makaranta ,but munasa karan zuwansu a satinnan"

"Eyyah Allah yakawoshi lafiya donjin gidannan nake uwa maka barta dabayanan" tafada tana karkade 'Yar zaninta tamike tabi bayan ummy ,Abby ma yafita.

#vote
#share
#comments
[8/19, 10:10 AM] Haisahhtttttt💅: 👠👠💅BAGIDAJIYACE👠👠💅

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace,joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

This page ix wholly dedicated to my besty Hameedart 🥰
Allah yabama mamanki twins,anty habiba saura karkice ameen🤩🤩

Written by
Hassenart

Littatafan marubuciyan:-

-RAYUWAR AFREDARH (Endless love)

-QASAITATTUN MATA

-RAMUWAR GAYYA (The shaded blood)

And Now

BAGIDAJIYACE

*Wannan littafin na kudine only #200 VIP #300 , idan kinbiya na ramuwar gayyya kibiya #100

vip #200.  Hanzarta kibiya kudinki kafin nagama*💃💃💃

5️⃣-6️⃣

*WACECE INDODO*

Indo Aisha diyace ga mal.abdullahi da mal.binta
Mal.Abdullahi asalin su fulanin  usulne 'yan asalin garin zuntu a wani 'kauye da ake kiransa fallanki,babansa ,shi yakafa kauyen sunan shi mal.yahya ,amma shidan kauyen gabane ana kiran kauyen *fallankin sab'a dutse*  to lokacin da ya bar kauyensu da matanshi ,sai yayi 'yar madaidaicin gidansu suka zauna anan.
sai ya zamana infulani sukazo wucewa zasu sauka awajen  sudanyi bukkansu na wucin gadi sutashi wasu su tsaya,ahaka waje yayi tayawa  har yazama gari ana cemasa  fallankin mal.yahya.

Mal.yahya yana da matan aure hudu dayara  Ashirin da uku ,Ashirin da daya matane biyu maza Abdullahi da Abdussalamu

Lokacin da yaran shi maza suka fara tasa wane yadaukesu yakaisu almajiranci abdullahi aka kaisa Zaria ,shi kuma abdulsalamu yafi kusa akabarsa a soba  .

Abdullahi Dane mai hazaka  saida yayi sauka sau uku da tishi ,abdulsalam baiyi dayaba. adon haka sai yafara sana'arn dinkin hula anan cikin Zaria ung. Albarkawa tunda ba halin komawa yabar dan uwansa bai dawoba,yina sana'ar sa yana karatun littafai  don sun zama gardawa.Ahaka wata rana wani alhj Ilu dake sayan  hula a wajen sa yayi masa tayin makarantan boko  ,bai wani musaba don yana da sha'awar karatun dama can,yaroki mutumin da yazo ya rokar mashi malamin su in ya amince.

Bai sha wani wuyaba sakamakon toshe masa baki da kudi dayayi.
Damakarantan  yaki da jahilci yasoma, daganan yawuce secondary yafara daga form 1 har 5 .lokacin har yafara sana'ar yadiddika da dinka Manyan riguna yana saidawa attajirai da masu sarauta duk da taimakon wannan alhajin

Koda yagama sakandire makarantan gaba yanema yasamu yayi diploma daganan karatun ya tsaya ,saboda hura masa wuta a kauyensu da akayi da yayi aure a lokacin tuni abdussalami yayi aure matansa biyu da 'yaya rututu.

Alhaji Ilu mai gidansa yasama  da maganar, yagayama duk matsalar da yake ciki,kwantar masa da hankali yayi  sosai yakarba takardunsa yasamar masa aiki a wani babban kotu dake a sabon gari.yakuma wanke 'yarsa  bintu yabasa   da kyautar  gida.

Hankali kwance yake gudanar da rayuwarsa  arziki na kara bunkasa har suka hayayyafa a lokacin da binta tahaifi yara biyune Fatima da ameena danginshi nacan suka matsa sai ya auri 'Yar uwansa yahadasu  inbahakaba,'yan Zaria zasu kwashe arzikinsa inya rasu,binta tanada sanyin hali batada hayaniya samsam .

Bata matsa masaba ya auro matarsa kuluwa  amma ana kiranta  yaya yabarta acan fallankin bayan ya Gina gidansa me kyau acan.

Tunda binta tahaifi 'yarta  Rahma haihuwar ta tsaya mata.bare kuma yaya da ko b'atan  wata bata tab'a yiba.

Tuni fatima da amina sun girma har anyi bikinsu ameena a tudun wada tayi aure da yaranta uku dayake gwarne takeyi itakuma fatima tabiyo mamansune danta kenan daya alokacin sunansa Aliyu a hanwa suka fara zama da mijinta cikin danginsa.
Itakuma rahma ansamata rana da wani dan Abuja yazo bautar kasa makarantarsu,suka hadu

Sai a wannan lokacin ne ciki bul ya bayyana ajikin  mama binta daabokiyar zamanta  yaya .

Akuma  wannan lokacin ne  mal.yahya Allah yayi masa rasuwa.

Suka d'ibi jiki aka tafi gaisuwa bayan an share zaman makoki an raba gado mal.abdullahi yayi shirin komawa Zaria ,nan enuwanshi suke shaida masa wasiccin babansa dayayi akan yadawo fallanki  da iyalansa da zama.

Yayi kukan bakin ciki bintama tayi ai wannan shi ake kira karkon kifi  daga cikin gari sai dosun kauye?

Adole yakara fadin gininsa yayi masu wadataccen gini na sumunti ,yaje wajen aikin su aka bashi transfer yadawo kotun zuntu.

Basudawo fallanki da zamaba saida sukajira akayi bikin rahma acan zarian amarya tatare agidan mijinta a abuja

Anan fallankin tahaifi 'yarta  aishatu danginta nacan nakiranta indo,itama yaya tahaifi danta namiji ana kiransa sanusi,sa'annine indo da sanusi wata biyu sanusi yabata.itakuma lokacin Fatima tana goyon 'yan biyunta sunba  indo wata hudu.

A lokacin da indo da sanusine suka isa shiga makaranta babansu  yasakasu a primary din cikin garin zuntu,kullum in zaije aiki zai tafi dasu.in lokacin tashi yayi yaje yadaukesu su wuce gida,a kullum cikin kawo masa kararta  ake yau taci abincin wane,gobe ta Zane wane, tankwalace original duk jarabawa ita ke daukan na baya.ancancanja makarantu  ba adadi amma Sam ba abunda ya sauyata nadaga kokari ko kawo kararta  kan yaran mutane

Dama kuma tunda indo ta taso , tun bata wuce shekaru ukuba tayi tanbari a unguwansu to, cizon yaran jama'ah iyaye na ganin ta ,suke dauke yaransu su Goya, ga rigima.

Watarana ne anty Fatima tazo garin da 'yan biyunta,shikenan tunda yara sukazo garin suka daina shan ruwan garin ko anbasu sai sun amayar,A lokacin basufi shekaru biyar ba,take suka fara rama.da tana kawaici ne saboda alkunyar dake tsakanin ta da maman matsayin ta na 'Yar fari ,bata ko kula 'yayanta bare ita kanta.gashi basuyi sa'ar kishiyar uwaba don Sam harsuzo sutafi daga gaisuwa ba maganar da zai sake hada su.

Ganin 'yayan mutane na Neman halaka abanza ,ai ba arziki tazari keyn motarta taje nemo masu ruwan roba a cikin gari,don tasan ruwan rijiyar garinne badadi kuma ita bazata iya basu narafiba.
Cartons 5 tasiyo dasu caprison datarkacen chocolate takawo masu. Aikoba ajimaba ,yara suka murmure suka saki jikinsu.
Saidaime?tunda indo ta kyalla ido taga ruwa ,tashi ga jida ,tana bama yaran makota da almajirai kwaf daya, saida takrar da duka ,itace kwabin wasan kasa dashi ,tajika jiki ta bannatar.
tun Fatima na kawaici harta kare dai ta tsawa tar mata.
Haba dan fadarda taima ta keda wuya ,tasami karkashin inuwa tamike kafa ta runtse ido taringa kwarara ihu iya karfinta,kaf saida ta tada hankalin gidan,kowa yazo lallashinta sai aga ido a soye ba d'igon hawaye.

Tun safe har karfe biyu tayi zufa sharkaf ,kowa dayagaji dole suka shige daki suka barta ,harsaida tayi su amai sannan bacci ya sureta a wajen.

Fatima da yaran ta kam tundaga lokacin suka fara ganin babi babi na izaya,shiga dubu fita dari saita jibgesu,don dole ta tattara kawunan 'yayanta suka koma inda suka fito.

Haka rayuwa tacigaba da gungurawa ,har indo suka shiga shekaru takwas,nan akeyinta
Don ita gabadaya tatasone tsundum cikin 'yan kauye bata San komaiba daga zuwa dandali sai taya kawayenta Fulanin dasuke zama a kauyen kiwaon shanayensu.
Tsabagen karfi dajin naci tuwon dawa na kangare har siyanfada takeyi.

Za'ai girkin engayu adakinsu zata fitar suyi musaye da 'yayan makota wai bata iya cimarba ,itadai tasha fate da sugar ba manja,dan gauda,tukurkusu dadai sauransu don haka tataso kakkaura gidirgir kakkarfa da karfi kamar shara'a uwa wani namijin

Tunda yaya tahaifi da namiji bayan dogon zangon da ta kwashe ba haihuwa ,shikenan gori ya ishi mama binta ,wai sune da gida ,waye waye......

Wataranar sallah ce kaf yaran mama sunzo da yaransu duk mazajensu suka kawosu,basuyo abincin sallah ba saboda nisa amma sun kawo buhunhuna da gallons na mangyada da manja da komai namahadin girki.

Mama wayayyiyace don haka dasauri tadaura babban tukunya taraya masu girki dayaji tsokokin kaji,tahada masu lafiyayyen kunun aya dayaji madara ta aika akaje zuntu aka nemo mata kankara tasaka aciki
Ta wanke lafiyayyun plates ,warmers da spoons tagoge ,tazuba komai tashimfeda dardumanta na alfarma datayo a saudiyya tashirya masu komai a falonta
Suka baje kwansu da kwarkwatansu,sukaja gara cikeda barkwanci da wasa da dariya kamar zuri'a daya

Takaici kam habaici dayada magana mama sun shata, ko kusa taki ko zuwa su gaisa saboda bakin ciki

mazan da zasu tafi,kowa da kudinshi na albarka,Rafa Rafa sule yaya ba tasamu ba,yooo basuma San da itaba.

Fitonsu keda wuya tajawo murhu tahada wutankara tafara mulla tuwo,tana wake wake: "duniya rawar 'yan matane na gaba yakoma baya"
Sarai sumama sun gane mai take nufi amma bawanda yatankata
Cikin sa'a saiga daidai daita tashigo a keken almajiran gidansu data ara

"6ii6itttttttt!!!
abani waje kar nayi 6anna,akaudakaya harnayi kutubal dashi alkur'an....."
Hango yaya tatakarkare tana tuka tuwo,kawai sai ranta ya kissima mata ta roreta da fada

Kewaye ta da murhunta tashiga yi da keken "agafara ba birki Yaseen"wani gigir,gigir tashiga yi da kan keken kamar zata duro ta jikinta,raba mata hankali yasoma yi jiri nadibanta,ga hucin tuwo,ga wuta gakeke da ke wuliwuli akanta.

" ke dan iyayen ki bar nan" tafada tana zare idanuwa

"Hajiya nakwalla shugaban aiki maza tukesa Tass,din vamusan guda...don dole ki tuke katon tukuny mu danna .....wooooo 'Yar aiki ke daya daya dagake saidanki sanusi mai kan jaki.....kinaji zaki kwashe ki kawo mana"

Yo kanta tayi dagudu zata daketa ,tako zille ta watsar da keken ckan tukunyar ,yako 6are cikin wutan,ji kake cuuuuiuuu!!!

"Wayyo jama'a gudunmawa ta shekarmun da tuwo" tasa hannu aka tana kwarara ihu ,cikinta ba kululu na azababben yunwa.

Lankwashe murya indo tayi sannan tayi maganar da karfi ,yanda kowa zaiji a aza indon keda gaskiya

"Wayyo yayan mu saida nace maki ba burki ....kiyi hankuri  bari naroko maki abincin en birni dakin mamanmu" tadaddalo mata ido tana mata gwalo da dariyan  sak'e

"Saidai ki roko wa uwarki dinmu bamuyi gadon rokoba" tanayi tana matsowa kusada inda take

Tsalle tayi taje kofar fita waje"haba Yar tsohuwa ,tarrr nake kallon ki.....kije jira zamanku da yunwa dan aradu babana  yau famfo zammai ga abinci gida baxai asaran kudi yabakiba......hahhhhh yau wata zataga malaikan mutuwa azzallaruruwa me wukaken azaba kala dubu"tafalla aguje tabar gidan

Vote
Share
Comment
[8/19, 10:13 AM] Haisahhtttttt💅: 👠👠💅BAGIDAJIYACE I👠👠💅

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace, joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

Dis  page ix dedicated to you my fanz 😍😍😍 indodo tace namiqa mata jinjinar ta gareku👍🏻
Allah ya bar kauna da zumunci🤝🏻

I reserve your comments my fam ,zanbisu daya bayan daya,ahankali zaku fara jin reply dina serially inshaallah,daga next update
amma sorry wasufa acikinkune , masu sharhi kadai zansa saboda groups din da yawa.
masu mun fatan alkhairi kuma da addu'oi kuma bazan mance dakuba  zanware maku page na musamman in jero  sunayenku, bayan next update.inayinku irin totally dinnan❣️💯

Written by
Hassenart

Litattafan marubuciyan
RAYUWAR AFREDARH

QASAITATTUN MATA

RAMUWAR GAYYA

_And now_

BAGIDAJIYACE

*Iittafina na kudine dashi da ramuwar gayya, anabiyar kowani daya #200,ake turowa ta katin MTN zaki turama wannan number 09065990265*
*Saiki screen shot a matsayin evidence ki turo,ko kuma zaki iya rubuto numbern katin ,ki turama numbern saman dai*

*Free page7~8*

Gidansu kawarta rahane tatafi,da sallama tashiga gidan kamar 'Yar arziki,ta gaida innansu rahane dake tuqe tuwon dare.
"Hannu innah ,shin rahane ko tana hiki?"
"Eh tana ciki ,tana shirin tafiya tallen gyada"
Cikin dakin takutsa kai batareda takuma cewa komaiba

"Kawalliya romon danga, kece haka se tsatso kyau kike abinki ?"

"To aminiya abun ai duk sirrine daka tsami nayi din wallahi innayi wanka ciwo nakeyi....(Hikicifffff,atishawa tayi sannan tace)wasa da ruwan sanyi" tafada tana maida 'Yar kwallan da yazubo mata sakamakon tarin da takumayi
"H'ummm lallai zanzo inhana mamanmu yimun wanka dakanta,kinga nima sai ,inayin irin naki....mene kikace sunansa?"
"Daka tsami,eh daka tsami sunansa kenan... Bake ba tsamin rana...bare kije talle aki saya"
"Hakane fa kawalli li, muje kar dare yemana a waje mama tayi fada"
Saida tagama shirga hau kanta a fuska nan tafito rangandau fuska yasha dige digen ba'ki baki dal da janbankinda 24hours ,angoggoga janvakin asaman idon maikon hambakin ya hade Dana kwalli. Sallama sukayi ma inna suka tafi,zuciyar inna fal murna domin duk ranarda rahane tafita da indodo tas kayan su,ke karewa.
Jerawa sukayi suna tafiya duk yaran da yagansu saidai ya canza hanya don ko da kuskure yaro ya biyo ta wajen su ,saidai kaje fahhh!,ta kafta ma da mari .
Suna isa dandali ,rahane ta aje gyadarta a wajen masu sayarwa,itakam indodo Ku tsawa cikin gantsara,gantsaran 'yan mata tayi dasuke fili da samarinsu suna rawa,tana shiga kowace maison kanta da mutunci tayi waje, itakam ko ajikinta don tasaba haka ake mata ,ita aganinta hakanma isuwace.

"Masu hid'i canja Mani,wannan baiyi mun ba"

Rawa takeyi duk Wanda akasa ta iya rawarsa tana rawar tana bin wa'kar
"Kin gani kin gani kwalelarki,shegiya 'Yar banza" tamaimaita wa'kar data canja masa ma'ana kadan daga k'arshe tareda shako wuyar wata da ke daga kusa da ita tahankada ta wajen filin.aiko saurayin ta yazaburo kan indo,tsalle daya, tayi tafita filin tafara gurza kafarta a turbayen wajen k'ura yaringa tashi fuuuuuu! Take wajen ya hautsine.'yan kida suka hau tattare kayan su ,suna Allah ya isah don sunsan ,sin rasa kasuwar ranar.

Cike da barazana da cika baki tahau yiwa kanta kirari,koya tsorata yakyaleta .kirjinta na dukan taratara ,yau kam karyana takare inani ?,ina wannan rusheshen basamuden " da wannan zancen zucin takarasa gabanshi, kanta tsaye" Waye yace dani baniba,shima ince dashi bashiba,saini tururuwa mai idon zalinci,taboni kaga tarandangi saini dakalin majina ahauni a zame, saini....."
"Ke yimana shiru kinjiko?" Yadaka mata tsawa,"ke kin zama mana annoba a gari ,mai kike taqama dashine?....yauto zanci ubanki inga abunda zai faru!"

Wani kururuwa ta dauka da kaf saida 'yan filin suka arta da gudu har budurwan da akeson taremawan ,can nesa suka tsaya yau su sha kallo ,kodai amauji bakin muguwa suji dad'i,ko kuma ayi mai lilis susha kallo .
"Kucasu arna kucasu,Ku casu bamai rabaku" aka dauka yimasu waka don a kara gingering dinsu

"Tab yaro bakasan halin indodoba yoo, kaidin ka yimun kadan a danbena,ai ina hada jiki da kai kwashe mun k'arfina zakayi tassss!, kagako baka isa ba" takarasa maganar tana ja da baya,zuciyar ta na rayamata ta arce.

"Aini abun kunyane indanbe dake saidai in lallasaki" yajuya yazugo tafasan bayan su

daka tsalle tayi tatimu a kasa"Nasama Ku d'auka za'a taba maku god'iya"tafadi cikeda sadakarwa.

Abun tsoro ,kawai zai akaji karan bulalai ya kacame wajen ,aka shiga zubama saurayin,ihu yake kwarara wa,yana burgima akasa yana soshe soshe,amma saukan dukan akeji bamai dukan.....

Haba a matukar rude indo taci hanya ta dibi kasa ta watsama kafar tata,"kafa mainaci banbakiba?kimun gudun da baki taba yiba" fil ta b'ace kamar barewa.

Tana barin wajen aka dakanta da dukansa jikinsa rudu rudu duk ya farfashe ,kowa watsewa yayi sai masu balain abota daahine suka rakube daga nesa daya yasoma magana
"Iluwa tashi don Allah, Yaseen kaima danaka, Dana gani babu tambaya kasan yarinyar nan tasuce,don ni tun ranar Dana soma ganin ta raina taraya mun. 'Yar ruwace to 'ya kyau haka....du Allah wata rana Ku kare mata kallo zakuga yanda kalolin jikinta kesauyawa....abunda yafi muzueawa sarauta Allah ido ,don Allah baya dauka ka banza"

Daya kuma ya maida kallon sa sama "Ku kuke ganin mu bamu muke ganinku ba,agafarcemu muntuba,minbi Allah munbiku....kuskure irin haka bazata kuma faruwa ba"

Duhun darene suka farga yasoma riskarsu ,su kadai awajen

"Iluwa ko ,ka tashi wallahi ko mu barka afadansu,mutafi" suka juya zasu tafi ,ai a sittin ya mike ,d'afff yaji kamar an zare radadin dayake ji a jikinsa,tsabagen tsorata.

Koda indo tadawo gida sad'af sad'af tashige dakin su tawuce 'Yar gadon ta .ta kwanta

Anty amina ne ta hango kafarta bututu da kura kamar wacce tayi kwab'in k'asa
"Mun shigesu Aisha kece haka?... Ji yanda sababbin kayan ki suka koma? Ji kafarki?...tashi don kaniyarki ,kije kiyi sallah"

Sum sum tamike ta. Fita kamar mutuniyar kirki,yo ita kanta tsoron kanta takeji,gani take uwa a mafarki

"Ciftsi Ameenah kinganta kuwa ai ta cika botiki tai wanka tukum,don wannan najasace ,bazata yi sallah a hakaba"Cewar anty fatima

" mtseww laifin mamane,abani ita tayi sati biyu a wajena ,wallahi saita kintsu...to ina bazasu bakaba"

Sai anan mama takada baki tace"wallahi nabaku go ahead, kutafi da ita ,ita kenan ba tabar tsoho ba bare yaro?, Sam baki biyo halinaba,yanzu kujira zakuji yanda gidan zai hargitse itada yaya....nidani ne bazan ringa biyewa jikan cikina ba.da in sun fara ana zuwa ,yanzu bamai zuwa bada hakuri"

"To algungumai,gulmata kikayi ko,ai yau zata gane shayi ma ruwane,ina me idon mayun take?" Dasauri anty Fatima taboyeta a bayan kyaure
Tagama waige waigenta,bata hango taba ta shige d'akinta ,tana 'yan zage zage,bawanda yace mata cikanki

Anty faty dakanta taje tayi mata wanka ta tsaya akanta tana alwala tana gyara mata. Har tagama suka shigo daki.

********************

Zau maganar fadan iluwa da indo yacika gari kowa yaji bai musawa yasan zata aikata,don abunda takeyi,inba shafar jinnuba bameyinshi bai ciwon jikiba. Amma ita kullum kamar kara Mata lafiya akeyi

Ganin sauyin  data gani a fuskokin kowa lamarin  yakuma burgeta ,tataka kowaye,bamai tankata.duk abunda ke faruwa ,bawanda yasani a gidansu har yayyenta suka gama kwanakinsu suka koma don tace bazata bi ameenaba,ranar dazasu tafi tunda tasha ruwan kunu ta arce,ba Wanda yakuma ganin keyarta sai dare lokacin tuni driven kowaccensu yazo ya kwashe su.

Wata makociyarsuce takira yaya gefe,watarana sunje gidan rasuwa, tagayamata rad'e rad'in da akeyi  akan indo wai ba mutum bace,saida takoro mata labari kaf ,sannan yaya ta d'age hanci ta rangad'a gud'a
"Wohoho Allah matubi,Ku shashashun inane?, indonce aljan ?, tabdijam yanzu naji nasamu lasisin jibgarta da hujjah"

"Adaibi a hankali innan  sanusi donko  lamarinta ba karya cikinsa, don yanzu haka iluwa nanan yana jinya....."

"Bayin Allah, kuyiwa Allah kufita daga waje ,komaji da rad'ad'in rashin damu kayi....."
"Dubu daga kinganmu a gidanki  shine har zaki koremu?" Yaya tafada cikeda jin haushi

"An koreku  d'in inbanda  rashin kamun  kai yazakizo gidan mutuwa,kina mana gud'a ?...Yaseen 'Yar uwan  zamanki  na kokari dake,don ma tanada mai maganin ki akusa ,bacin haka dakin cutarda hakurarran baiwar Allah"

Ainan  bakin yaya yafara tururi,bakin cikinta daya,anyabi kishiyarta anzageta,cikin kumfar baki tahau bala'i .da kyar mata suka rabasu ,don suna daf  da dakuwa.
don itama abokiyar fadan babayabace.
nan dakyar aka jata  suka fitar daita daga gidan.

Wayyo ina wuta tawatsawa mama binta da indo,  nan komai yakuma jagulewa,kullum cikin bala'i gidan yake ,don yaya tana cewa tak!
Inbai gamsarda indo ba ,saita ramamasu.

Ana haka indo da sanusi suka gama primary, ba laifi tafara kokari don takan dauki na Ashirin haka cikin su sittin.
Kuma alhamdulillah tasama  admission a makarantan day maza da mata na zuntu.

Akuma  hutun datasamune ta shirya kayanta anty faty  taturo ,aka dauketa  taje tayi masu Hutu kafin sigama registration.

Vote
Share
Comment
[8/19, 10:13 AM] Haisahhtttttt💅: *👠👠💅BAGIDAJIYACE👠👠💅*

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace, joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

Story and written by✍🏻
Hassenart
☎️090- 659 -902 -65

*Basai na maimaita kaina ba ,littafin nan na kudine #200 ne kacal zaki turo mun ta wannan number 09065990265,  VIP kuma #300 na katin MTN, kibiya kudinki don more karatun littafin ki a tsananki*
👏🏻

*Free page9️⃣-🔟*

Saida tashake Ghana must go biyu taf  ,dakaya .tunda tashigo dasu cikin motar gaba daya annurin fuskar idi driver ya dauke,sakamakon tsamin kayan datti da warin ajiya da yagauraye kamshin turaren motar saida tazo har tashiga motar metatuna oho!, tafara jijjiga hannun budewa,tana shirin karyeta,azabure idi  ya zagayo ya bude mata,ranshi fal takaici,don inba cin akan aikinta yazo wannan garin da ba abunda zai hana ya jibgeta kamar Allah ya aiko sa,k'wafa yasoma yi sannan ya d'an
Sassauta murya yad'an rankwafo cikin motar ta windon waje"hajiya yadai,ko akwai abunda kika mantoshi ciki ne"da lalatattan hausanta tasoma bashi amsa"uhm'u uhmum rahane,k'awar arziki na manta bamuyi sallama ba hine ,yanzu ta hwad'o mun a rai ,kaga yazamammun tilashin wuya nadubo ta"wani malolon abune yazomar makogoro ya toshe,dakyar ya iya maida yawun bakinsa,bayan yad'an kauda kansa, jin wani irin mak'ak'in warin kore fet din bakinta dake barazanar d'aukemasa numfashi don inbaicikaba k'ila ta shekara batayi brush ba.    Yinaji yana gani takuma fita a motar ta arta cikin unguwa ,ba'ajimaba saiga su tareda wata matashiyar yarinya da zasuzo sa'anni duk'u duk'u da ita ,k'afa bako takalmi.har gaban motar ta

rakota"indona wazai ringa taremun fad'a inkin tafi" wani wawan tsawa tadaka mata"keeee!, to saiki gayyato uwarki tatare maki,tukunama waike dak'ik'iyar inace,na'aza nan nagama baki shawaran yanda zaki daki banzaye,yanzu kinamun maimaici ,salan inje zaria intarar 'yar farfesun nawa yagaji da jirana yahuce ya sandare....malama dan janye tsumman jikinki saura karki kwaso takalmi kisa kibari indawo insameki hakan"
"Wohoho! Indo waike wannan kawarkice ko 'yarki,kitsahirta mata hakamana ,ke kuma da azaban kwadayi 'yan uwanta dakike gani yasakike like mata tana maki gori da wulakanci..."
Yayace tafito daga cikin gidansu ,jin karad'in indo dayacika layi,tafito taga dawacce takeyi.
"Ahayyye ,cas lallai,inbaka mutuba ,ba zaka daina ganin abun haushiba ,kekuma asuwa?, karuwa a masallaci?" Idi driver ne da kuluwa suka dauki salati atare "indo nice karuwan?" Mere baki tayi,bako d'ar aranta "ohoo tanan kika biyo to kilan hakanne...malam zakaja mato mutafi ko in kwashe tsummokarai nane inkoma ciki? " jinjina kai yayi cikeda gajiyawa ikon Allah "hajiya kiyi hak'uri  d'an yau se allAllah shirya" baibi takan surutanda kuluwa tacigaba dayiba,ba kwama bare fullstop ,tasai fad'an tsaf ,don tuni rahane tasulale ,don tasan indo na jin zuciya zata fincikota tajibga.
Wuta yabawa motarshi yaci hanya ,yanbin kwazazzabon hanyoyin,duk in yashiga inzai fito saidai kaji k'ummm! Indo tak'ume , nan zata haujaraba bazata yi shiru ba zatajita takuma wani k'umuwar,zagi kam drivern nan yasha ta har sukafito titin zuntu.
Goshinta duk sunyi k'ulayen azaba,shikam duk tsiyar datake cikanki baice mataba. Basuyi nisa da tafiyaba ,barci ya sureta bata tashi farkawaba saida suka shigo Zaria.
Mik'a tayi tahau mitsike fuskarta da kwalliyar kwalli da janbaki datayi  ya hade da zufa yayi dameji tadawo kamar aljana bakaganin komai sai farin kwarar idonta.
Tunda  ya hango idonta tamadubin dake kusa dashi yake guntse dariya duk wannan kwalliyar haukan yadame guri guda,bata wani damu da murmushi dayake yiba .tsaki tamayi"mtseewwww,Allah yara bamu da motsatse"
Kanzil veceba saima shan kunu da yayi, shan kwana roundabout din p.z din da taga yayi a maimakon adauki hanyar hanwa shi ya tsoratar daita,shalll taga driver yadauki  hanyar shiga GRA din gadan gadan,awani zabure  ta k'walla mai wani gigitataccen k'ara a kunne , dagudu yataka wani wawan burki ,sakamakon kambin motar da ta nemi kub'ce masa a hannu. Aguje yayi parking a gefen hanya.
"Hajiya lafiya dai?" Tsaki tayi tafara babballa masa harara kamar aljana
"Ina fa lafiya zaka kaini inda za'ayi gandar kaina,kahe  kai, in d'an yankan kaine,inbahakaba meyakawo mu nan,muda zamu unguwarsu.... Yo kodai kadauka bansan wuri bane,kana wani wuri wuri da ido kamar ifiritu,ja'iri tsokan kaina yafi karhinku ank'ur'an..." Takaicintane yacika mai zuciya don dai idi driver badai fushi ba
"To dan gidanku ,yanxu ya kikeso ayine?ko kibari inban kaiki gidan su hajiyanba daganan saiki nema hanyar matsera,dan inkika sake mun ihu aka saina karairayaki nawatsa ma karnukan layin nan Yaseen"
"Iyeee!, wata kan anty tasan kuna cin naman mutane,tokodai harda wannan mijin nata,dama ni tini nad'ibiya masa ayar tambaya, wannan talliyar kan nasa kamar na yahudu da nasara,to mujed'in inga dame kuke tak'ama,koka d'auka zan firgitane?, to aradu k'wank'waman kaina sunfi k'arfinka..."figar motarshi yayi a mugun zuciye,zuwa cikin GRA din ,don duk ak'agare yake ,yak'osa yakaita yahuta da jarababben surutunta maras kan Gado

Adaidai wani mahaukacin gida,taga drivern yana karkata akalan motar ciki,horn yayi tareda kokarin shiga harabar gidan bayan ankwaye get d'in. Wani hamshakin gida mai cikeda furanni da bishiyoyin kwakwa tagani  yacusa kan motar ciki,sojoji birjik acikin gidan.tsurewa tayi take tahau sunbatu" lahaula walakuwata,ya bagabaga ya kilu ,wabillahi labinnasi ...idirisu ina zaka kaini ne? Daga wasa...aradun Allah wasa nake maka,mama na sona araye...nabi allAllah nabika ka maidani gida nafasa zuwa gidan su fatsiman..."
"Kinfasa,gayyato mitsa mitsankan naki? Bagidaji kawai to har gaban dodon tsafinmu zankaiki ,sai naga ya zuk'e jinin jikinki zanfita" nan yashiga da motar wajen adanasu,yayi fakin  yafito
"fito haka nan nace" zare gwalagulan idonta tashiga yi,hawaye na diga
"Yaseen banfita,saidai kakirasunan..." D'age kafad'arta sama yayi"to ki tazama ni kinga tafiya ta"
Daidai nan ta hango anty faty cikin shigar dandatsatsiyar leshi,sai walainiya takeyi ta hasken rana.
K'uri tayi da idanuwanta cikeda tantaman in antyn tace.da dariyarta takaraso ta bude mata kofan"autanmu sannu da hanya"ja dabaya tayi saurin yi su Hassana da Hussaina ma suka juya a zabure cikeda taraddadi,kwalla ma idi kira tayi
"Idi mai yafaru ne,ko iskantane suka bugeta a hanya?" Sauke wahalallan ajiyar zuciya yayi
"Kamar kinsani hajiya,naci wuya a hanya ,kar ala naimaita"
"Allahu sarki ,gaskiya naga fuskarta kamar daddawa sai dango takeyi ga jirwayen hawaye faceface.... Topah ya zamuyi kenan" zaraf Hassana tasoma magana "mommy akira kakkarfan kurtun can Joseph mana,sai yadauketa ashigo daita daga ciki"
Indo datun d'azu take jab'e kamar kayan wanki ba uhm bare um'um rungume da tarin kayanta ,jin an anbaci soja yasa tazabura tafito a sittin  .hanyarda mom suka fito tanufa a tsiyace,karo tayida kakkarfan kirjin wani dake tunkaro cikin compound din,tipp tafadi 'kasa cikeda jin jiki................
Wani kakkausan muryane  yasoma amsa kuwa a kunnenta
" Waye wannan? Hassenorh wata bagidajiyace wannan? "

Like
Vote
Share
Comment
[8/19, 10:14 AM] Haisahhtttttt💅: *👠👠💅 BAGIDAJIYACE👠👠💅*

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace, joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

Story and written by✍🏻
Hassenart
☎️090 -659 -902 -65

*Dedication*

*Wannan page din sadaukarwane gareku  masoyana,🌹🌹 kuyi duk yanda kukaso dashi mallakinkune,saikunso wani ya karanta. 'yan groups d'ina masu nuna mun tsananin 'kauna ta hanyar turo mun zunzurutan comments 'dinku ,masu karamun k'warin gwuiwa,nima ina sonku kamar raina*
*•••HASSENART FANZ GROUP •••*

*•••RAMUWAR GAYYA/BAGIDAJIYACE COMMENT BOX•••*

*•••RAMUWAR GAYYA FANZ GROUPS1️⃣&2️⃣•••*

*My warm regard tareda jinjinar bangirmata baxai tab'a yankewaba agareku HASSENART NOVELS PAID GROUPs  1 & 2.      Koban fad'aba kundaisan  ance babbar masoyinka shine Wanda zai baka kudin shi don ya nishad'antu da labarin ka,don haka nima inayinku totally alqur'an🤪💯*

~*Littafin kudine books d'ina wato RAMUWAR GAYYA da BAGIDAJIYACE, only #200 na katin mtn .sai kuma idan VIP kikeso #300 ne shi,zaku turo katin ta wannan number 09065990265.*~
~*Hajiya karki biyoni inba biya zakiyi ba ,don aradun Allah zan blocking d'inkine nan take👌 *~

*Free page1️⃣1️⃣-1️⃣2️⃣*

Kecewa da dariyar 'keta su Hassana sukayi har suna duk'ewa a wajen don sunsan dai batazo gidan a sa'a ba tunda Allah yayi mata gamoda farouq.

girgiza kai mom tayi,sannan tawaigo tak'are ma umar da indo  kallo.

"Umar wannan yarinyar dakake gani
Kanwarmuce,itace autarmu..."

Dafe k'irji yayi kamar Wanda yaga abun tsoro "mum,wannan abar ?...jitafa kamar bugun aljannu,nifa dafari na'aza gamo nayi...tabdi lallai wannan inhar kanwarkice,amma zama daku baisa ta gogeba tabbas ba k'aramar cikakkan BAGIDAJIYACE ba..."

Murmushi mum tayi don ita batafaye son hayaniyaba.jinjina masa kai kurum tayi
"In boy yazo katambayeshi relationship d'in dake tsakanin shi da ita"

Mikewa indo tayi cikeda masifa jin ankirata da bagidajiya tayi mai k'ur da dakwadakwan idan uwanta uwa na mayu,ai dasauri ya kauda fuska,donshifa rod'i rod'i yaga tana masa a ido ,tuni ya soma ganin jirijiri.
"Malam bar ganina haka ,kazata kanwar lasace,to kwarankwatsa nasaba danbe da shirga shirgan mazan k'auyenmu dagani sai guntun fatari ,bare kai me kamada tsinken sakace wani korekore dakai zibun cutar shawara, don haka kashiga  cikin hankalinka inkuma saimun gwabzaneto"

Tsuru yayi mata da idanuwansa kamar yana hango wani najasa ajikinta. Kanzil yakasa  cemata

"Hahahhh cabd'i yau yaya ba magana ne ?...gakafa ga indo,Ku d'ab kafta musha kallo don Allah" Cewar Hussaina kenan.

Juyowa yayi a mak'uran zuciye  don gidanku yaushe nafara wasa dake ne?...bar wajen nan kar na b'arar dake" simsim tarab'e tawuce  ciki. Hassana ma bin bayanta tayi dasauri don tasan yana iya zanesu yanzunnan .dama ita tuni mom tashige cike tabar su anan
Dawowa takan indo yayi datayi  tsaye akansa tana jijjiga jiki
"Ke kin d'aga mun takalmina kinban waje nawuce kokuwa?k'afa kamar na tsinnaka"
Jan zogala zogalan kafarta data take masa takalmi tayi ta hankad'a  masa takalmin gabanshi,tana faman ballare ballare  tareda murguda masa baki.

"Mtsewwww,Toni me zanda  takalmi nan har ake mun tsawa kansa ,takalmi sai kahe  na hilanin garin mu"
tajuya tashige ciki,sai ya ??tana saka k'afarta a cikin falon da sauri tayi saurin dawo da kafarta wajen ,nan tasandare tsaye daga bakin k'ofa
"Ya rasulullahi manzan tsarki,jama'a inane hanyar dakukabi Nene?kut macizzai🤔"
 Dakatawa da tafiyar farouk yayi da azamansa yadawo wajenta  ,d'an nesa da ita ya tsaya,cikeda zullumi, yana toshe hancinsa yana k'arewa rafkeken falon kallo
" ke ina macizan?" Bata bashi amsaba saida ya zauna ,dab'as tayi a kasan varendarn tukuna.sannan ta bude baki hagaga tasaki 'katon hamma ,barufe baki bakomai tana gama hamman ta hau tofi da yamu tagefe,jikake tuftuf!

Jiyoda kansa tad'aya barin yayi,sannan yasake mata magana cikin tsawa tsawa
"Ke wai bakiji mai nace bane?"
Zare d'ankwalin kanta tayi zuwa gaban goshi tahau Sosa gashin kanta da akaima kitso 'Yar Hausa(two hands) tsabar dadewa har ya daskare baka iya ganin tsagon kitson,sai uwar k'ura

kamar an barbad'a,wani hamma  takuma yi harsaida tayi hawaye cikinta yabada kukan"k'uuuuuu" saida tashafa cikinta sannan tace "mai rogo....uhnm ,wai mekahe,macizzai ko?To eh maccizzai mana ni ,narasa ta inda sukaine, suka wuce ta wagga waje,sufa sukayi ne...yayane oho..."
"Ke wai macizan ?" Yafad'i a matuk'ar rud'e .Tab'e baki tayi
"malam bari inmaka gwari gwari,don naga kai din kamar bagidaje kake jinka... Tambaya nake ,shin ta ina ake shiga gidan saman Canne?...don dai kaga kasarnan kwalba ne,tekune menene allahu a 'alamu"tawatsa hannuwanta a siket din jikinta ,yaraffff.

"Mtseww ,nikike kira ma da bagidaje? Kodayake ba laifinkibane,tunda ga tayil kina kiransa teku?kaini wata jarrabtane yasameni ma,natsaya nake daka tataki?"

Juyawa yayi zai tafi,ai asittin tadank'o rigarsa."bawan  Allah temaka muni kasadani da d'akin fatsime,kahin sanyin wajen nan yamaisheni k'ank'ara,bakajiyo ihun cikina daganan?....to Yaseen ko Karin safe banyi ba zumudin zanzo inci farfesu.....ko ka kwatantamun yanda kuke haye wannan wajen"

Daura hannu a goshinsa yayi kafin yafincike rigarsa dakyar
"Kedakata,wai wajena ne kikazo?, to bara inkira boy yazo yashigar dake"
yana magana yana maida numfashin wuya don tsamin jikinta ne yaji yana yin k'urin sashi amai,wayarsa yaciro yayi dialing wani number,ringing biyu aka d'auka

"kai haidar kana inane? ....ka Yiwa girman Allah kazo karabani  da wata halittar....eh gamunan anan main door...tom"

k'arar k'ofar wani glass shi yadawo daita duniyarmu.bayan talula dunuyar tunani......

Takowa aliyu yayi da sauri fuskarsa fal fara'a
"A'aaah indororos ne yau a gidannamu?"

Kyar tayi mai idonta nakan sawayensa, saida ya karaso kusada su ta sauke numfashi,
"Gadanga ,karka gaya mun gurin nan ba tekubane?naga ka keto lakadan"

"Haba indo ,tayil dinne yau tazama sabo  a wajen ki? "

"Ohooooo,kace mun sumuntin turawa,to ai naga wannan harda ratsin ciyawoyi,gashi kuma ina kallon idanuwa ta ciki.....shi yasa nakid'ima,gidan nakune kamar na masu cinkai..... "Umarne ya tsinketa ta hanyar cema aliyu yawuce shi.

" hmmm d'an daudu  Allah yakiyaye hanya kayi mun taimakon....Allah yabaka macen kirki Irina"
Kwashewa da dariya,haidar yayi"aboki kace kazama d'an daudu"fusata yayi yajuyo a hargitse kamar zai kaimasa hanb'ari

"Kai karka gaya mun badadi kajiko?"
"Toohh,lallai katunzura dayawa,to ke indo me kika gani a jikinsa kikecemasa d'an daudu? (Yafada yana kamo hannunta sama)....sai anjima inanan shigowa.... Yanzu dai bari inji da bak'uwata"fita yayi cikeda takaicin wannan bagidajiyar indon .

Itakam indo sakin jiki tayi tafara kwararo mai surutu,ransa fal dariya badamar yi don gaba d'aya tazama kamar wata dodanniya.dakyar ya taitayota suka shiga cikin falon ,da sukazo hawa steps kuwa ,saida sukayi nisa tawaigo ,ai sai ta nemi rikitowa." Subhanallah rike nan mana"yanunama inda ake rikewa ,amma ina santsin silvern da zufan hannunta ,yasa hannunta tahau zillewa.karshe dai da rarrafe ta karasa shigewa ciki.

Alokacinne kuma mom tafito jin shiru ,bataga
K'yallin  indo ba.gurus tayi tareda Rike baki "aifa namanta auta batasan gidaba...ji yanda ake taitayoki,sai kace tsohuwa"
Hussaina ce takaraso wajen
"Hmmm yaya haidar dama ka kyaleta ne,mugani juyawa zatayi ne?...ai nida Hassana na muna hangota ta window"
"Hussaina autan kikema haka....ko ,aidaidai daku take .bata bukatar atare mata"

"A'ah fatsima kefa kikejanmun raini,Sam basa ganin girmana, gadanga kadai kece mun ,anty shi yasa,nakeshimasa albarka akoda yaushe"

"Vassu kinji antyna ta kaina ni daya nama isheki,baki bukatar tadan yuyuyu" yadai lallabata suka shige ciki.don yalura ana dab da tsiyacewa itada Hussaina.

Vote
Share
Comment
[8/19, 10:14 AM] Haisahhtttttt💅: *👠👠💅BAGIDAJIYACE👠👠💅*

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace, joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

Story and written by✍🏻
 Hassenart
☎️090 -659 -902 -65

*Dedication*
*pejinnan nakune 'yan k'asar nijer musamman 'yan damagaran da Agadaz.kuyi duk yanda kuka so dashi,tukwuicin soyayya🤸‍♀️🤸‍♀️🧚‍♂️*

*Ina 'yan nijar masu buk'atar biyan kudin Littafaina ,sun rasa yanda zasuyi,Ku garzayo Da shirin biyan kud'inku,donko 'Yar uwanku tabaku solution don ita tuni ma tabiya nata,karki bari abarki a baya inkin shirya  Bini ta p.c*

Aradun Allah ink d'ina yafara gigir-gigir🙄,don haka ina dab da gama free pages, wainda kuka biya kunhuta,keda baki biya ba #200 ne ake biya na katin MTN sai a turama wannan number 09065990265 ,inkuma VIP ne #300.

*Free page1️⃣3️⃣-1️⃣4️⃣*

"Waikai haidar yanzu kai har zaka iya rayuwa da wannan bagidajiyar yarinyar a gida d'aya,kui using spoons da cups daya ?....h'ummm,katab'a k'arema hak'oran bakinta kallo kuwa?abu very greenish dagani baisan yanda ake gurza mai brush ba....haba gaskiya in nine wallahi daina mu'amala da komai na gidan zanyi har sai tatafi,innemi sabo kawai"

Sukuti haidar yayi batareda yatankashi ba,don shi harga Allah yana son Aisha, kuma baya iya ganin laifin ta don shi komai natama dariya yake bashi,kawai ya dauka yanda mutane ke mu'amalantarta shi yakesa take muzantasu in return...

"Abokina bakace komaiba ?"
"To mezance ,kadaisan bazan tab'a nunawa k'anwar mom ,k'yamaba....so aje magana tagaba kawai"

"OK nafahimceka,aliyu kanuna mun akwai banvanci tsakanina dakai ko ?,ai shikenan"
Azuciye yabar masa d'akin yayi ficewarsa,shi adole ya gaya masa magana
"Mtseww kahad'iyi garwashin wuta k'arewar zuciya...."
Jin shiru bai dawo d'akinba yasa yatashi ya nufi gidansu,shima.

************************
"Wohoho ya shafi ya kafi,yau wallahi zasu kashe mu da yunwa,aradun Allah banna iyawa..."
Jan k'afarta tayi har kitchen d'in gidan ,iya ladi tagani tazage tana soyan plantain,wani takaici ne ya zo mata wuya ya k'ume ta

"Hod'ijam,menike gani hakane wai?, kina sane bayin Allah naji ranki da abinci kinzo kina soya ayaba,uwar me zakiyi dashi?iyeeh tambayarki nakeyi,koko silar mugunta da k'eta?...

kina cinnaro mun wa'innan 'yan micimicin idonuwan naki kamar k'wark'wata....hmmm yo gida babu dole azo nan anasoya ayaba gobema lemo zaki soya kenan ko...dake nakeyi"

Damuwane ,ya bayyana k'arara a fuskar iya ladi,batasan sanda tasoma yi mata magana tsawa tsawa fad'afad'aba

"Ke waike,wacce irin ja'ibace...kinzo kintasani gaba da sassafe kina cimun fuska?kamata nakusa jika dake zakina tsinata....to hirrrr d'inki donko inada marasa kunya irinki agida ringis,waenda zasuyi mun maganinki....
Maganar abinci kuma ki had'iyi hanjin cikinki,inbazaki iya jira k'arfe goma tayiba..."

"Caskalin kanbura'ube,nikeke zagi haka,yau zankoyama uban bakin nan naki hankali inyaso kya iya kiran me rama maki...."

Juyawa iya tayi tacigaba da suyan plantain d'inta ,irin tabarma banza ajiyarta d'innan

Cikin rashin zato tafyallota ta kafafunta ,jikake timmm!,kanta ya k'umu da kitchen cabinet, kafin k'ugunta yadaki k'asan tiles d'in wajen.

Wani k'ara ne na azaba ta k'walla,wacce batasan yafito ba.hakan Wanda saida yaja hankalin ilahiran mutanen gidan buuu,sukayo hanyar kitchen d'in,inda suka juyo k'arar

Waige waige tashigayi kamar zararriya ,can Allah yabata sa'an hango ladle agefe,dasauri tasura tasaka acikin mai d'in ta tsamo plantain d'in da tafashen mangyad'a yaroyaro,tayo bakin iya zata d'ura mata shi haba,kankaceme tuni tanemi zugin datake ji a k'eyarta tarasa, tafita a atamanin ,tana kururuwan Neman dauki

binbayanta tayi da spoon d'in, daidai sunfito sukuma da zuwan su farouk da aliyu,ai da gudu suka take masu baya.

ganin zasu kamota bata fansheba,yasa tayi watsi da ladle d'in plantain d'in mai cike da mangyad'a, tafinciko rigar iyan tabaya,daga daga tayi zata fad'i...

Daidainan farouk yazo bai saurari komaiba yashek'eta da mari.

Wani kururuwar ihu tasaki kamar zata cire masu dodan kunne
Tuni muryanta ya d'ashe,Nan tahau danna mai ashar kamar jikan maguzawa

Iya ladine datasha da k'er ta tsaya tana falaifalai da baki,tana karkad'a jibga jibgan albarkatun k'irjinta wanda suke har cikinta.tana lankwashe murya tana bashi hakuri,adole antare mata d'innan,tasamu fada.

Batai auneba saidai taji tayi kukan kura tayi caraf ta cafki nonuwarta.da duka hannayen ta biyu

lilo takeyi kamar tasama jaka,dama ga abu zudun zudun kamar jarka,

kururuwa iya tashiga yi ji take kamar za'a yage mata k'irjin .

Salati da sallallami su baba me gadi suka d'auka lantai maishara kam dariyarta takeyi son ranta,don ita bata tab'a karo da irin salon fad'an indoba ,dama gashi sunada jik'ak'k'a da iya ladi.

Anyi juyin duniya tasaketa tak'i saki ,saima k'ara damk'arsu datayi uwa tasamu igiya.sukuma gasu maza ba abun su rababa,ita me rabawar kenan lantai ,tayi gefe abinta tana dariya.

Ganin ba sarki sai Allah, yasa farouk ya finciki indo tagaba,aliyu ya finciki iya tabaya

Nan iya tawatse yaraf a wajen kamar tsumma.
"Jama'a kukallanmun kirjina nonuwa na sunanan,ko sun fita?"

Indo nadak'wak'wo gula gulan idonta ta je gabanta ta tsaya tana numfarfashi,"don uwar mace tasake yi mun magana...alkur'an sainacire ma mutum hanci ...kinyi sa'a ba wuk'a kusane... Dakin sha yanka,nid'in nan dakike gani cikakkiyar 'Yar dabace,ina jiran yaran naki darabon lakhira tayi bak'i"

"Lamarin ashe babbane,tabbas kwalwar yarinyar nan ba lafiya" cewar farouk kenan cikeda al'ajabi

Ganin shikaran kansa ya jinjina ma al'amarin yasa ma'aikatan gidan dayazo kowa yafara ja baya yina sulalewa,kar tama hango fuskar shi ,bugun jujunta,nagaba tayo kansa.

I needs more and more comments so,
Vote
Share
Comment
[8/19, 10:15 AM] Haisahhtttttt💅: *👠👠💅BAGIDAJIYACE👠👠💅*

*©HIKIMA WRITERS ASSOCIATION*
*(Home of peace ,joint entertainment to educate and enlighten our readers)*

Story and written by
Hassenart
☎️090 -659 -902 -65

Happy marriage life💞
Nafeesah,Allah ubangiji yasanya albarka acikin auranku,yakauda duk wata fitina,yabada dawwamamiyar zaman lafiya,da 'Karin k'aunar juna,yakawo zuri'ar da al'ummar annabi (s.a.w) zasuyi alfahari dasu.
Congratulations dear🤝

*Last free page*

*Daga wannan page d'in pajin kyauta ya k'are ,duk wacce takeso kibiya kudinki ,ki karanta #200 zaki biya na katin MTN zaki turama wannan number, 09065990265* *saiki screen shot as evidence ki turama wannan number dai*
*Inkuma VIP kikeso #300 ne, shima wannan number dai nasama  zaki tura mawa*

1️⃣5️⃣-1️⃣6️⃣

Indo kam tunda tashiga gidan zaman lafiya yayi masu k'aura,yau da wannan gobe da wancan basu samu arzik'iba saida anty safiya takwasheta tamaidata garinsu saboda admission d'inta na cigaban karatunta nagabada primary yafita

Iya ladi kam tanaji tana gani haka tunda suka sami wannan matsalar da indon,dole tahak'ura tabar aikinta.
Don tace watarana indo zata iya d'aukan ranta.kowa yayi jimamin rashin ta don dai ba laifi suna jin dad'in girkinta,amma daga baya suka share aka sama wata da zata maye gurbin na ta.
************************
*WANENE UMAR FAROUQ*

Umar mak'ota suke dasu haidar anan GRA dukda dai dama tun su haidar na hanwa kafin su dawo nan d'in,Abokai suke ajinsu d'aya a makarantansu tundaga Js 1 suke tare har ss3
So,lokacin da suka dawo GRA sai sukazamo makota nan shak'uwarsu takuma k'arfi har

yazama komai tare sukeyi cin abinci ,kaya iri d'aya komai don hatta bacci baya rabasu,don idan wannan yaje gidansu wannan ya kwana yau ,gobe wancan zai je gidansu d'ayan su kwana,abotansu shi ya had'a kawancen iyayen su suma .
Farouk su biyu ne rak wajen iyayen su,shi da k'anwarsa maryam maryam sa'oine da en biyu.

Baban farouk major general ne a NDA don haka,koda suka gama secondary takardunsu kawai yakarb'a yanemar masu NDA .
shi haidar da fari bayason soja amma farouk nason yagaji babansa,kuma baison su rabu,dole yacanja ra'ayin abokin nasa ,haidar yabi bayan abokinsa aka Neman masu navy acan d'in yanzu haka a wannan shekaran suka shiga .
Farouq jarababben yarone,ga miskilanci baison magana mai tsayi balle hayaniya

Tunda indo taje gidan ya janye jikinsa da gidan saidai haidar shi yaje.
Bai saki jikinsa da gidan ba saida yaji indon tatafi.
********************
Indo anshiga makaranta cikin nasara,anfara karatu cikin farinciki gunin ban arziki,kafin daga baya komai ya kwab'e.
Tazamar masu bala'i a makarantan k'ungiyarsu akeb'e yake na zallah marasa ji maza uku sai ita da aminiyarta rahane.
Basa shayin tab'a koma waye harta 'yan ajin gaba dasu in sukayi cacan baki to ranar hanyar makarantan in an tashi zama yake kamar filin badar tsabagen rigima,tunda set d'in su indo suka shigo makarantan seniority yawatse ,kowa yasamu liberty yayi duk abunda yaso.

Akwai gonakin mutane ata bayan makarantan suma kaf sun gallazesu da sata daidai da masara saisun karye masu sun gasa inbeyiba su zubar.6arna yadda kasan 6eraye.
Ba laifi tana d'an k'ok'ari tunda daman bawai batada k'walwar bane rashin maida hankali ne.
Saidai kuma me,tunda tashiga makarantar ta bud'e sabon salon tsinin balaga ga rawa uwa mazari duk kalar wak'ar dayafito ta iya rawarshi.
Tuni tashiga sahun 'yan gaba gaba a Hausa club na makarantan su,daita ake zuwa makarantu fadan rawa don aciyo Kofi.
Kad'an kenan da aikin indo
*******************
*CIGABAN LABARI*
"Haidar bi iznillah yau a gida zan kwana...I missed ma mom"
"Kaima kafad'a haka bareni....ni danake so har zuntu inje a hutun nan...kawai ka shirya zuwa anjima mubi motan dady"
Harhad'a komai nasu sukayi ,suka gyara ko'ina .very important abubuwan su suka d'auka a jakan bayan su na sojoji,daganan Zaria tayi kira.basu shaida ma kowa ba saidai kawai gidan sukayi masu tsinke .gidansu haidar suka soma sauka,nan gida yarikice da murna "gasu yaya,gasu yaya" lokacin indo tanata baccinta batasan bidirin da akeyiba
Suna sauka basu tsaya 6ata lokaci ba suka shige gidansu farouk ,basu kuma fitowa ba saida sukayi wanka sukayi sallah don har abinci acan sukaci.sannan koda suka dawo farouk d'akin haidar ya tafi,shi kuma haidar ya wuce sashen dadynshi ,dayake dawowarsa kenan.

Indo da farkawanta barci labarin dawowar haidar ya risketa
Ai da fyallelen zaninta tayi sashen shi dagudu.
Gab da zata shiga tafara slow tunawa da abokinshi datayi,"kardai suna tareda wannan mai k'irar samudawan... Mutum kullum fuska gintse sai nace an aiko masa da sak'on mutuwar uwansa?... To wannan karon da cikinka nazo kana mun kan kara zan idasa maka Dana gumagumai"

Sand'a tasoma yi,ta tura k'ofar a hankali,cikin d'akin ta kutsa kanta tsaye,me zata gani.....

Farouk tagani kwance shemesheme a katifa daga shi sai boxer da singlet,gefen sa laptop d'insane yana kallo ,Sam hankalinsa yayi nesa a kallonsa baisan ma tashigo ba dayake yabama 'kofar baya

Wani irin gurnani ne ke fita tajikin laptop d'in.
Daddalo idanuwarta tayi waje ganin mace zir da namiji suna aikata masha'arsu ,suna wani irin murning kamar kuraye.

K'ara ta k'walla mai aka tafita da gudu,hanyar bq tayi

Dafarko yaso share ta ,amma yana tuna surutunta ya zabura ,yayi cikin BQn da gudun gaske shima don bai fatan ta tons masa asiri and she can do that....

Caraf ya damk'eta ,zare ido ya hauyi waiko y furgitata.

"Ke dan gidanku meye yasaki gudu har kike kwalla mun ihu aka?"

Ware duk idanuwarta tayi tana kantara masa rashin kunya

"Abubuwa marasu asanin kyan dubiya... Hmmm andai d'uma abun kunya...."

Borin kunya yahau k'okarin yi

"Ke lallai kinada aljanu,ko kuma kin fara kur6awa,inko ba hakaba,kije ki kuma nazari ....nida kika shigo kika sama ina istigfar .....zaki sa mun magana?"

"Sankaci?     Ashe haka kuke mazan bunni?...ina kallonma idona ace bahaka bane.....koda yake ba laifina bane ba nakaba ....kasan inada laluran jinnu ,gasuda hegen tonon silili